# NA GASKE

Mounkaila Hamadou GANDOZI
Niamey, 2002

Ay na gane
Don ni ne
Kake zanga zanga
A kan tituna
Ka iya sani fa
Ni ne a ka zaba
A yaw ni a ke ma tambari
Ni,da parti na da kundi sa

Ka iya sani fa
Ni ne a ka zaba
A yaw ni ne a kema molo
Ay nima sai in dandana
Ay nima sai aljabba
jampa da wando na shadda
Har ma akala da turkudi
Da koufa da minbar ta zinari
Ni ma yaw sai guidan bisa
Sai marsandisi
Ga en kunnay da sarka zinaria ga matata
Yarana sai makaranta na kasashen turay
Dangui,en uwa da aboken a cikin liyapa

Ka yita sukuwar makamniyar kuralka
A yaw ni a ke ma tambari
Kundin dokokin kasa a hannuna
Sojoji da maaykatocin koti ni ga ikon su
Ni ne doka,ni ke milki

Ka iya hankuri
Ko gobe kay ma a zabe ka
Ni dai tasar nono nike
Gobe in sha kindirmu na
Jibi in ci cukuna
Gata ma
Sai dai wani ikon allah